DAME AKE ADO part (1)

1Mahaukaciya yarmacukule mahaukaciya tasaci zare dandazon yaran da suka zagaye mahaukaciyar ke ihu suna fada yaukam adurkushe take tana kuka tarike cikinta sabanin canbaya da idan suna wannan wakar take rawa eyehuuh eyehuuh kuka takeyi yau babu rawa suka kakama fada suna ihu malam sulaiman dayake dosowa tundaga nesa yacika yacika dataikaicin yanda yaran unguwar suka takurawa matar dababu wanda yasan daga indatake kawai an wayi garine anganta a unguwar yadauko tsumagiya yayi kansu yafara dukansu sai suka watse sunaci gaba da ihu dawakarsu filin yazama sai ita kadai harlokacin tana durkushe tana kuka

2ya isa gurinta yana fadin baiwar Allah tashi kitafi abinki kinjiko wayyo Allah cikina mutuwa zanyi maganar datafito daga bakin mahaukaciyar kenan wacce tasanyashi kara kallonta da mamaki dan tsawon wata tara dayasan matar baitabajin tayi maganaba saiyau kuma abin dayabashi mamaki baiwuce jin maganar tata yau irin tamutumin dayasan ciwonkasa baceba kafin yakai gacewa wani abu yakuma jin tace wayyo Allah zanmutu saiyaga jini yanazubowa ta karkashinta dasauri yace subhanallahi haihuwa ce zakiyi dandama tanada ciki wanda akezargin wanine yayimata akan bolar datake kwana tabayan gidan malam sulaiman din baiyi wata wataba yakamota dasaurinsa danjin kamar tana nishi ga yaran basu bar gurinba sai ihu suke tayi yaciccibeta yakaita soron gidansa dake jikin bolar ya tura kyaure

3soron yanufi cikin gida dasauri yana kwalawa matarsa kira Deeje Deeje sukaci karo tana tahowa dasauri takalleshi Ify malam zomuje mahaukaciyar nan dake kwana akan bolar nan tajikin gidan nance babu Ify ina tunanin nakuda cetakeyi subhanallah muje mlm tafada atsorace sanda suka karasa soron tabbas nakudace takeyi bari nadauko zannuwa kirawo Lami acikin gidansu mama yanufi gidansu Lami wacce yakasance soro guda akeshiga cikin gidan matar kanin malam dince yafara sallama daga bakinkofar da zata sadaka da gida nasu

3soron yanufi cikin gida dasauri yana kwalawa matarsa kira Deeje Deeje sukaci karo tana tahowa dasauri takalleshi Ify malam zomuje mahaukaciyar nan dake kwana akan bolar nan tajikin gidan nance babu Ify ina tunanin nakuda cetakeyi subhanallah muje mlm tafada atsorace sanda suka karasa soron tabbas nakudace takeyi bari nadauko zannuwa kirawo Lami acikin gidansu mama yanufi gidansu Lami wacce yakasance soro guda akeshiga cikin gidan matar kanin malam dince yafara sallama daga bakinkofar da zata sadaka da gida nasu

5Allah zaitaimakeshi mlm din yafada cike da matsananciyar damuwa ko ajikinta wai antsikari kakkausa sai ma cewa tayi gaskiya saidai kayi hkr amman bazan iyatabataba abinda akace wurinda akahaifi shege ka taka kaida arziki har abada nidazakuji ta tawa ma aidakunfita daga soron gidanmu kada tashafamana talauci karabuda ita malam kaje kasamo mota akai matar nan asibiti zubar jini tayi yawa tafi don Allah kada ta mutu malam din yayi duru duru sannan yafice dasauri yajanyo kofar lami tayi tsaki takoma cikin gidanta tana cigaba da fadin Allah daiyakawo mlm wlh waje za.ayi da ita bazata goga mana talauci ba daman kulum anata fama sai anfita asamu dakyar ita dai Deeje kamo mahaukaciyar tayi dake tafadin wayyo cikina

mutuwa zanyi
6deeje tace kinga daina cewa wayyo kama salati ringa kiran sunan Allah Aikuwa cikin ikon Allah mahaukaciyar takama kiran sunan Allah dakarfi deeje tana rike da ita tadinga wani irin wani irin nishi saiga katon da deeje tace insha Allah sauraki mahaifa daure kiyi nishi kozata fado takama yin nishi da karfinta deeje tafara fadin subhanallahi ahankali zakiyi Amman ina yitakeyi da iyakar karfinta sai deeje takula ba ita takeyin numfashinba daga Allah ne kawai saigigice ta rude ganin mahaifar tafado jinin kuma yana bulbula kamar fanfo dakyar ta iya janyo yaron tayanke masa cibiya jin yana ihu daidai lokacin mlm sulaiman yaturo kofar yana fadin deeje gamai motar nan kota haihu ne cikin kuka take fadin shigo mlm shigo kaga halinda take ciki yaturo kofar yashigo kallo daya yayimata

7hankalinsa ya dugunzuma yakama cewa da deejan kamota muje Asibiti deejan nakokarin kamata sai dai mahaukaciyar tariko hannunta tana fadin mutuwa zanyi kada kukaini asibiti kuwahala sunana Asma.u haki yakamata deeje takuma rudewa tana fadin innalillahi kifadi gidanku wacece ke maimakon ta iya cewa wani abu sai kalmar farko da deeje ta ambata ta innalillahi wainna ilaihi rajuun raiyayi halinsa talangabe anan hankalinsa deeje da mlm yayi matukar tashi deeje tafashe dakuka tanafadin mlm munshiga ukku hankalin mlm sulaiman yatashi jikinsa yaduki rawa duk yarudema yarasa abinyi deeje ce tace mlm kasanar da jama.ar unguwa sukawo mana
8 dauki Allah yasani niyyar taimako mukayi mlm yanafadin dole saimun sanar da hukuma kulada yaron da gawar bari na je nadawo kafin takara cewa wani abu yabazama yafice tatsugunna tana kallon yaron daketa wutsil wutsil cikin zani kyakkyawa gwanin bansha.awa son yaron yafara shigarta Lami taleko tana fadin yaya tahaihu ne tayi turus cike da tsoro tana kallon mahaukaciyar saita dafe kirji tanaci gaba da fadin badai tamutuba deeje wane bala.i kuke shirin kawomuna wlh babu ruwanmu takoma dabaya deeje tadaga kai tana harararta ranta abace amman tagaza cewa komai don takaici
9tana nan zaune tsawon minti arba.in tajiyo karar jiniya tamike jikinta yana bari jin datake bata taba shiga police station ba amma yau ga motar police harkofar gidansu tana nansaiga mlm sunshigo dayan sanda ukku kowanne dauke da bindiga daya dagacikin su yakalli mlm sulaiman yana fadi mlm katabbata abinda kafada shine gaskiyar magana wlh babu kari ko ragi Allah yana kallona mlm yafadi dasauri har lokacin hankalinsa tashe dansanda yagirgiza kai yana fadin duk dahaka zamu tafi dakai da matarka danzamuyimaku wasu tambayoyi deeje tawaro ido tana fadin nashiga ukku don Allah yallabai kayimini rai wlh bantaba shiga irin wannan
10motarba yakatseta kada kidamu hjy bawani abu zamuyikiba tambayoyi kawai zaku amsa jiyo karar zuwan motar yankwana kwana suka kuma rudewa haka nan akasanya mahaukaciya deeje rungume dayaron suka fice daga gidan cikin rakiyar yansanda Lami tana labe tana lekensu ta kofa tana dariya tana ganin sun fice tafara fadin Allah yakara maganinku masu neman suna kenan banda haka daga ganin mahaukaciya tana nakuda har wani kinkimota kukawo kamar kukukafi ubankowa imani koda yake ai neman sunane kuma kunsamu tamurguda hannu ta tafa acinya tana juya idanuwa sanda suka fice jama.ar unguwar sun fito cirko cirko ana kallonsu kowa da abinda yake fada mlm jibrin yashigo gida fakan fakan cike da tashin hankali yana kwalama matarshi kira Lami Lami
11DAME AKE ADO ......Tafito daga daki dasaurinta tanafadin mlm lfy wannan irin kiran kamar

zaka tsagan dodon kunne yakalleta cike datashin hankali yace jinayi ance yansanda sunzo gidanmu sunyasheku gabadaya Anyi police station daku wai antsinci gawa agidan tarike kugu tana kada kafa A.a bakarya bane gaskiyane saidai ba.abaka Ibr dai dai ba andaitafi dayaya da deeja dansu suka debo ruwan dafakansu kamar yaya kinanufin yanzu shi yayan da deeje suna can wurin yansanda? Dagaske kenan Ansami gawar kaibakacin ribar zance wlh katsaya nagayamaka yanda Abin yafaru mana
12DAME AKE ADO Baikoma tankawaba hartasanar dashi duk Abinda yafaru tadora dacewar danhaka nibaganin laifin yansanda wlh sunyi daidai kokai yayakagani? Yadansaki rai yana fadin nasha gayawa yaya wannan halin nasa watarana saiyaja masa masifa gashinan kuwa mutum yace kofada yaga anayi saiya raba can yaje yakarata idan naga abin yayi tsananani naje nasarwa da Abokinsa mlm Habu bani ruwa nasha nakoma kasuwa yakarasa magana yana haki
13DAME AKE ADO Malam sulaimai da deeje suna zaune agaban tebur din DPO kusan awannisu shidda kenan apolice station din DPO yadaga kai yakallesu shikenan malam tamutu kada kadaina taimako domin ladanka yana gun Allah yanzu zaku wuce dayaron gobe zamu turo wasu jami.an namu zasu amsheshi amikashi gidan marayu Allah yasaka da Alkhairi Ran mlm yayi fari yamike daidai lokacin damatar tasa ta mike itama tana fadin babu damuwa ranka yadade dahaka sukabar ofis din deeje tana rungume da yaron suna isa gida deeje tadora amurhu tawanke yaron tas wanda yayi kuka haryagaji malam yasamo zam zam da 14 DAME AKE ADO ...Dadabino akabashi yasha sannan ya kuma yasiyo madara irin tagari akajika masa da ruwan zafi yasha saigashi yakama bacci Auwalu da sani diyoyin deeje sai murna suke wai ansiyo musu yaro akasuwa sun sami kani mahaifiyar tasu dariya kawai take musu tana rungume dayaron dayake kuma shiga ranta duk bugun dakika mlm yadawo daga masallaci yataddata rungume dashi yayi dariya yana fadin Deeje uwa kenan ki ajiye dannan koyafijin dadin yin bacci tayi dariya tana kwantarda shi agado tace wlh mlm jinyaron nake kamar nice nahaifeshi yayi dariya yana zama sallamar malam jibrila daga bakin kofa takatse musu hirar tasu mlm sulaman yatashi dasauri ya leka yana fadin jibrilu yaya akayi ne? Free Mode See
DAME AKE ADO part2.
Jibrila yagyara tsayuwar sannan yace wani Ibr nakeji yanzu gurin Lami danadawo wai ankaiku police station amman yaya ka kasa aikawa agayamani ai da na biku naji abinda yafaru yayi dan yake yana fadi gani nayi ba wata babbar bace ba shiyasanya ban Aiki maka ba amman yanzu komai yawuce da izinin Allah to Aishikenan Allah yakiyaye gaba amman dai yaya karage halin nan naka watarana zai iya janyo maka adaureka mlm sulaiman yayi murmushi yana fadin kayya duk Abinda da Allah yakaddarowa bawa babu makawa saiya sameshi Amman kuma dai yaya ance gidan da aka haifi shege masifu suna sauka acikinsa yanzu baka gudun abinda zaije yazo madaukakin mamaki yaziyarci mlm sulaiman yadinga kallonsa baki bude da ................ Dakyar yadaure yace A wanne hadisin ko ayar kaci karo da wannan batu Ya kama sosa keya na rashin madafa yasan halin yaya nasa sarai zai iya yimasa wankin babban bargo dan haka ya wuce dasauri yana fadin aishikenan Allah dai yasa ruwan sama yawanke mana daudar yabishi dakallo har yakule sannan yaja tsaki cike da taikici yakoma ...Dasafe tun Asuba Deeje tadora ruwan wanka ta wanke yaron tas tasanya masa kayan jarirai mlm yashigo tana rungume dashi tana bashi madara a filinboti ya kama kuwa yata zuka yakalleta tana dariya yace tomasu amsar yaron sun iso kishirya muwuce akaishi tadaga kai takalleshi nandanan hankalinta yatashi yakula

dahakan danhaka yayi sauri yadauke kansa yafice GIDAN RAINON YARA Ankammala duk rubuce rubuce da dakaura hotuna harda na gawar Asma.u mahaukaciya mlm da deeje zaune gaban shugabar gidan tana tana musu godiya takirawo wata cikin ma.aikata data amshi yaron wanda harlokaci deeje take kankame dashi dan angama bincike ta goyeshi abaya ma.aikaciyar jinyar tayi tsaye kikam tana jiran deeje takwanto yaron amman taki mlm sulaiman yadan zungureta yana fadin kwantoshi mana deeje sai tamanne kafada suka zubamata ido da mamaki sai kawai tafashe muru dakuka mamaki yacika kowa agurin shugabar gidan takasa magana tana kallon ikon Allah koda yake takula dayanayin deeje tunda suka shigo bakuma yaune tafara ganin irin hakaba saidai amatsayinsu na.ama aikata bazusuturawa mutum da baisanya kansa ba dangudun azabtarda yaron nidai dan Allah Abarmini yaron nan tunda kunada su dayawa mlm sulaiman yadibeta damamaki Allah yasani abinda keransa kenan amman kuma baisaniba ko anayin hakan ba shugabar Hjy Amina tayi dan murmurshi gami da komawa takwanta jikin kujerarta tana fadin daina kuka malama deeje zamu iya barmiki yaron nan saidai akwai wasu sharudda da zamu gidayamiki 19 wlh nayadda da duk sharadin da zaku gindayamani takatse shugabar cikin hanzari Atake anan shugabar tagindaya musu sharadin amsar yaron suka amince harda sanya hannu a rubuce sunrabu da shugabar akan duk wata guda zasu dinga kawo yaron anaganinshi da haka sukayi sallama cike da jin dadi suna tafe ahanya deeje takara kankame yaron tna dariya kai mlm da.ankwace yaron nan dasainayi jinya yaron dashi rai yake wlh yayi dariya yana fadin ke kam da baki taba haihuwa ba da anshiga ukku kin kankame yaro kamar zaki maidashi ciki to barka da mlm wane suna zakasanya masa kuwa Ta tambaya Aubakiji sunandana fadi gurin cike takaddunba koda yake lokacin kin rude aitinjiya da daddare nayi masa huduba da AHMAD 20 idan Allah yakaimu ranar sunansa ta zagayo sai ayanka hakika ayi radin sunan A masallaci gurin shayawar ne dai nake tunani yanda za.ayi tunda kina dauke da cikin wata ukku bamu sani ba ko zaiyiwu kishayar da shi amman dai matambayi malaman Asibiti tayi ajiyar zuciya kuma kaga na shekara ukku rabona da haihuwa sai dai mu shayarda shi madara siyo madarar shanu yakama ka kenan kullum tana dariya to yaya na iya tunda Allah yabani da haka suka isa gida cike da nishadi lami tana jiyo sallamarsu takwasa da gudu tana lekowa sam basu kula da itaba tarike haba cike da mamaki ganin sun dawo dayaron abayan Deeje dan haka takuma tabbatarwa har cikin gidan taleka taga sunata shigowa dakayan arziki wanda hjy Amina tahado su da shi tayi musu Alkawarin zata dinga zuwa tana dubashi 21 don Ta amshi Adireshinsu duk da sunce zasu dinga kaishi din sanda jibril yadawo yatadda Lami a cunkushe ya tambayeta abinda ya faru saita fitittike tana fadin sai dai azabi daya azaman gidan nan ko ni ko shegen yaron can sunfa dawo dashi dayaya zamu yadda murayu da shegen a gida yagyara tsayuwa yana kankance ido don Allah kada ki gaya mini zancen banza inace da safe suka tafi da shi kina nufin sun kuma dawowa dashi tagalla masa harara to zanmaka karyane ka shiga gidan nasu kagani mana kuma da alama da shirin zama ya dawo don nagansu da siyayyar kayan jarirai kala kala ya shuri takalmi cikin bacin rai yayi gidan yayan nasa ko sallama babu suna tsakar gida azaune deeje tanayiwa Ahmad gashin cibiya 22 Malam sulaiman yadaga kai ya kalleshi da mamaki yana fadin Ify dai jibrilu kashigo babu ko sallama yasamu guri yazauna yana muzurai ramsa abace yace kayi hkr yaya rainane abace nashafa.a jinayi ance wai kadawo dashegen yaron nan me kuma yadawo yi? Ransa yabaci amman yadanne yace ba shege yakeba sunanshi Ahmad kuma yawuce wai tunda hargashi nan kana gani ana masa gashin cibiya haba yaya wanne irin tonon siline saikace baka taba

haihuwaba idan karin ya'ya kakeso basaikaje kadauki nawaba ko kuma kaje kauye kadauko wasu ba Amman saika bige da dauko shege nagayamaka kada kakuma kiransa da shege kajiko kuma naki daukar naka dan ko kuma nakauye shidin dainakeso idan kuma kaine sama dani sainaji marar kunyar banza .........23 irin naka duk wani abu dazaka aikata na Alkhairi saiyazamana kaidashi kake gaba wannan yaron kasan iyakacin baiwar da Allah yayimasa to tsaya nagayamaka daga yau yashiga cikin 'ya'yana zan kuma rubuta wasiyya ko bayan na mutu araba dukiyata kashi shidda Abashi kaso daya don Allah baihalasta Wani yagaji wani bane ba danace yagajeni jibrilu yayi shiru cike da takaici don yasan halin yayan nasa akwai fada idan kataboshi danhaka yamike sumi sumi yang fadin Aishike nan nidaman inaguje maka illar da akace zama da shege yana kawowa ne inji ubanwa aihar yau kakasa kawo mini hadisi ko ayar datace hakan nakuma gayamaka kadaina Ambaton dana Ahmad dashege kajiko yakarasa ficewa yana gunguni babu yanda zaiyi

24 malam sulaiman yacigaba dafada sokon yaro sai mace ta huroka kazo kana yiwa mutane fiffika daga ganinka wannan bara.ayinka bane ba matarce taroshi shakiyiya kawai deeje takwantar da murya tana fadin karabudashi Lami kam saidai Ayimata Addu.a matar da yaran gidan bata bariba balle wannan mudai Allah yarayamana shi cikin Albarka yakoma gida cikin borin kunya yatadda lami tsaye tana jiransa yana shiga tatareshi yaya kukayi dashi? Yasamu guri yazauna yana dafe kunci yayi tsaki yana fadin bakiji yanda yabalbaleni dafadaba kamar wani ubana harfa cewa yayi bazairike dana kona wani dangi sai wannan shegen ke har doka yakafa min waina kiransa dashege ma tayamutsa fuska tana fadin maganinka kenan mara zuciya saunawa nake gayamaka kadaure kayi gidan kanka muhuta da mulkin mallaka dan wannan dakin biyun dayabamu ke rudinsa dayasanan kana da iko agidan aida baiyimaka haba saikayitayi kada ka mallaki nakanka kayita zaman karoro 25 Ahmad yataso yaro maicike dakwarjini da hikima da basira wanda kowa ke kauna. Duk inda yazauna zakaga ana sonsa iyayensa suna nuna masa gata kullum yana cikin yan uwansa suje islamiyya da dare kuma suzauna kofar gida saida rake ko mangwaro saidai tunda yatashi ya kula da tsangwama da kyarar da Lami da mijinta ke masa ga wani suna dasuke yawaita kiransa dashi shege amman yakula har sauran yayyansa da kanne Lami bata kauna saidai sanda yayi shekaru ukku yagano azabarta ko ahanya suka hadu saita rankwasheshi musane abokinsa a gidan kuma sa.ansa tasu tazo daya sauda yakanbishi gidansu wasa kamar yanda shima yake biyoshi amman duk sanda yabishi saita azabtar da shi har wuta ta tabawatsomasa wata rana kuwa ta kulle abandaki wai wuni guda mamanshi na nema har kuka tafarayi tadinga zagaye unguwa sai gab da magriba ta hankodoshi yasha kuka majina damiyau lokacin yanada shekaru biyar sanda mamansa tagansa tarungumeshi tanafadin

26 Ahmad dina inakashiga kaida nasanka bakada yawo cikin muryan kuka yake fadamta innarsu musa ce takulle ni abandaki wai saina shaki kashi namutu narasa abinda nayimata ta tsaneni Ummata kigayawa baba yasake mana gida mana tausayin yaron yakamata tasha bala.i da Lami akan yaron tun yana da wata ukku da Auwalu yashiga dashi tashaka masa ruwan kumfa ahanci har kusan dambe sukayi tundaga tadaina baiwa kowa danta ga tirtsetsen cikin haka zata goya abinta haryayi shekara ukku saita ajiye kaninsa Rabi.u tasungumeshi abaya don haka rigimar tayi sauki yanzu kuwa yawuce goyo duk irin tsakanin mlm dayimusu takiji hakanan dai rayuwa taci gaba da gudana cikin wahala da azabar Lami shidai jibiril baya dukansa Amman baya ko kallonsa don yace masa baffa saiya dokamasa harara yau ummansa

tadawo awo abakin Asibiti saita siyowa kowa kayan sanyi da mlm yabata sallahu duk tashi tafi kyau don hoton dan bal din nanne maradona daman shi yana da son bal don haka yasuri tashi yayi waje da gudu kai tsaye gidan jibril yashiga yana kwalawa abokinsa musa kira musa yafito daga daki aguje mahaifiyarsa na kwalamasa kira Amman baitsayaba saida yadangana datsakar gida inda Abokinsa Ahmad ketsaye cikin farin ciki da dariya Ahmad ke daga masa rigar yana fadin kalli yaro babanmu ne yabaiwa umma kudi tasiyowomuna kalli harda maradona ajiki shugaban yan kwallo duk randa zamuje filin bal da ita zani kaikuwa bakada ita musa yatsaya turus cike da takaici saiya saki kuka mahaifiyarsa tafito daga daki dasaurinta tana fadin tsinanne shege dukanka yayi ko? Yagirgiza kai yana fadi a.a badukana yayiba riga babansu yasiyo masa maihoton maradona zai dinga yin ado yanafina kyau nadaina zuwa filin kwalloma adaki zandinga zamana jikin Ahmad yayi sanyi yakalli abokinsa yamika masa rigar yana fadin kada kadaina zuwa don Allah garigar tawa kadinga Ado da ita yamika masa saidai tuni mahaifiyarsa ta warce tana fadin Banza soko aibada riga ake ado ba kaga wannan tanuna rigar ana saidata akasuwa da uba ake ado wanda shikuma ba.asaidashi akasuwa kasha kuriminka wata rana ko rigar gwal da zinare yasanya yafita saiya tsani kanshi don baida rigar Ainihi ta mutunci tawurgawa Ahmad rigar tanacigaba da fadin dauki tsiyarka kawuce shegen banza watarana zakagane Abinda nake nufi hankalin yaran gabadaya yatashi duk basu fahimci komai azance ba
yakwasa da gudu ganin tayi kansa da ice gadan gadan saida ta kaishi har babban soro sannan takoma yanufi gidansu jikinsa sanyi kalau yana hawaye Ummansa tafito daga daki dazummar dora girkh taci karo dashi zaune shiru gabanta yafadi don tasan yarone mai kazar kazar da wasa tabbas bashida lfy takara dasauri tana kiran sunansa manya yaya na ganka anan zaune shiru meke damunka yadaga kai yana kallonta idonsa yakada yayi jajir saita kuma rudewa tace gayamini meyake damunka cikin shashshekar kuka yace innarsu musa ce takoroni don naje nunama musa rigar da babanmu yace kisiyomana tayi ajiyar zuciya wato dai bazaka daina shiga gidan nan ba kadaina kajiko yadagamata kai Alamar to sannan yace Amman idan musa yakwalamini kira indan leka amman kada nashi dakinta ko? Abin yaso bata dariya wata irin shakuwa ce tsakaninsa da musa wacce bazata iya rabasuba dan Allah ne yahadasu da daddare suna barbaje atsakar gida suna cin abinci cikin tsakiyar hasken farin wata tuwone da danyar kubewa wacce tasha kifi Ahmad yakai katuwar loma bakinsa yahidiye tadakyar yakalli Ummansu tasu yana fadin Umman wai meye shege ne? Gabanta ya yanke yafadi matuka tawaro idanu waje
........... Cike datashin hankali can kuma saitayi saurin dakewa takwantar da murya tace banace kadaina tambaya irin wannanba Ahmad meye Amfanin wannan tambayar inace a makaranta malaminku yace kudaina tambaya akan duk wani abu dabayada Amfani gabadaya duk tarude jikinta har rawa yake ganin haka yasanya shima hankalinsa yatashi don baya son yabatawa ummansa rai yace kiyi hkr umma nadaina daman innarsu musa ce naji kullum saitace mini shege canake ma suna ne Ashe magana ce mara kyau ma takuma Rudewa tace kadaina damuwa idan tace haka idan akace da mutum shege aiyayi wata gwaninta ne yayi dari.a yana fadin natuna har kika hanasu cewa hakan ko? Tace yauwa yarona ashe kagane ka daina damuwa idanta kuma cemaka kuma kada na kuma jin kalmar abankinka kada kuma ka tambaxi wani ko malaminmu tunda kaga nagaya kako yace to umma bazan kuma tambayaba sannan yacigaba dacin Abincinsa tayi wawiyar Ajiyar zuciya cike dafargaba saitaji duk Abinci yafita

daga kanta magabadaya tabbas dole mijinta yadauki mataki akan wannan abin idan bahakaba saidai tabar gidan da yaranta dantayi Alkawarin har abada bazata gayawa Ahmad wayeshiba saboda hakama tunyana dansheka ukku tadaina kaishi gidan rainon yara shugabar makarantar ce kezuwa taganshi har gida har sanda tabar aikin agidan rainon yaran takanzo ganinsa saboda tana masifar sonsa itama hartadinga danasanin barinsa agurinsu din gashi babu damar ta amsheshi a lokacin dadaddare duk yaran sunyi bacci ta tashi maigidan nata wanda shima haryafayin bacci yatashi cike da mamaki da fargaba don tun dayamma yaga ranta abace nakula tunda maraice akwai wani Abu dakike boyemin to kinshiya fada kenan yanzu tafashe da kuka tana fadin aidazun mabakin gaya maka haka kawai ba sai don gudun kada yaransu ji Abinda zamu tattaunawa to wallah nagaji dazaman gidan nan na.amince kakamini haya da masifar da ake shirin kunno mini saita kara fashewa da kuka batunyau ba nake sanarda kai irin azabar da matar nan takeyiwa yaron nan Ahmad ba har Abin yakai nadaina sanarda kai toyau takai har Lami kenunuwa Ahmad shi shege ne bazan yadda ba Allah wannan neman masifa ne dason tozartani Hankalin mlm sulaiman yatashi yadinga fadin subhanallahi garin yaya hakan tafaru tasan kuma doka ce nasanya agidan nan tunba yauba ko mijinta nace yafadi wannan maganar zamuraba gari dashi

29 DAME AKE ADO ....... ........... Dasassafe yatura yaran makanrata safe kamar yanda suka saba duk Ranar Assabar da lahadi da babu boko saisu tafi daukar darasi amasallacin Unguwar kaitsaye suka shiga gidan jibiril sunyi sa.a kuwa yaran gidan suma sunfice sai matar gidan zaune akan tabarma suna ta hira suna jin sallamar su mlm suka daga kaida mamaki dominsunsan baya shiga gidansu saita baci jibril yamike yana fadin A.a yayane sannu dazuwa zauna mana yadaga hannu yana fadin ba wannan takawoni ba gargadi nashigo yiwa matarka duk da nasan kasan duk abinda take aikatawa to wlh ahir dinta hawainiyarta takiyayi ramata Lami ta dafe kirji tana fadin nikam nashiga ukku nazama shara komai aka kwaso sai ayaba mini yanzu kuma nayi..... Rufemin baki marar kunya banza aikinfi kowa sani Abinda kikayi waike danbakida mutunci harkike tsare yaron nan Ahmadu kina masa habaici dole duk saiyasan shiba mune iyayensaba ko? Lailaha ilallahu nidin wlh sharri akemin yaushe nataba tareshi nagayamasa wannan maganar kuma? Yakalli deeje yana cigaba dafadin gayamata duk abinda tafadi tasan ya dawo kunnenmu deeje tamaimaita duk Abinda Ahmad yasanar da ita har shegen datake cemasa sai lami tayi wuki wuki babu kuma bakin magana dontasan tafada yanda kuma suka tsara sai take tunanin ko deejen taji nema
-------> DAME AKE ADO part 3.

30 Malam sulaiman yace to yaya koharyanzu sharri ake miki eye? Mijinta ya amshe don Allah yaya kayi hakuri kuskurene akasamu kuskuren gidanku nace kuskuren gidanku tun yaro nan yana wata guda matarka ke cutar dashi yanzu kuma abin yanzu kuma abinda zata koma yi kenan idan kinkwantar da hankalinki watarana zan sanarwa Ahmad wacece mahaifiyarsa kodon yadinga yimata Addu.a ma amma sai sanda ya mallaki hankalin kanshi yatara iyali yasami wadanda zasu debemasa kewar danginsa amman ayanzu banshirya sanardashiba don banason hargitsa masa rayuwa yakasa karatu da.anfanar rayuwarsa idan kuma bazaki daina ba zan saida gidan mukoma haya kowa ma yahuta don daki salwantarda rayuwa Ahmad gwara na kare rayuwata ahaya har Abada kana jina yanuna jibirilu kaine mijinta banason jin makamanciyar wannan magana a gidan don Allah yaya kayi hakuri wallahi tadaina insha Allah

baisaurareshiba yakalli deeje yace maza wuce mutafi duk sanda yakuma sanardake irin wannan maganar datafito daga bakin Lami kisanar dani nikuma za.aga hukunci dazanyi wlh suka wuce suka fice Lami tabisuda harara tanafadin aikin banza ko kunya bayaji mace tasakoshi agaba yazo yana jaraba kaikuma takalli mijinta awulakance saiwani rawar jiki kake kana bashi hkr yana kara kumbura to idan ancemasa shege shin karya akayi? Yanada uban tsinanne dan mahaukaciya insha Allahu sainayi Ajalinsu aitsintacciyar mage bata mage yau tundasafe gidan babu dadi gurin samarin gidan dasuka fara mallakar hankalinsu domin tunsafe Ummansu batada lfy
A Iyakacin shekarun Ahmad sha ukku da sani shabiyar da Auwalu shabakwai rabi.u shabiyu sunfahimci nakuda ce takeyi tunsafe yan uwan maman nasu mata keshige da fice anyi su tafi makarntar boko sunkasa zuwa alokacin Auwalu yanada shekar karshe sani yana aji hudu Ahmad yana aji daya hakama Rabi.u dayake kusan tard akemusu komai donsun tashi kamar yanbiyu cankamar daga sama suka farajin kukan jariri suka mimmike a rude suna lekawa amman sun kasa fita sunajiran Abasu izini saida aka kammala gyara uwar dajaririyata sannan akwala musu kira har rige rigen fita sukeyi ganin Umman tasu tana zaune akan filo afalo kamar ba ita ce tahaihu ba tayi kyau sai kamshin turaren wuta ketashi suna shiga ta washe baki cike da farinciki tana dariya inna balkisu kanwar tace tace Albishirinku samarin umma Atare sukace goro inna tayi dariya tanafadin yara saikunbani tunda nayi muku albishir yar budurwa da.aka haifa muku wacce kuke marmari amakota sasuka saka ihu atare saida umma ta kwabesu sannan suka natsu suka dinga amsar yarinyar suna kallo duk wanda ya.amsheta baison baiwa dan uwansa saboda kyan yarinyar Ahmad kam kamar jira yake su fito yakwasa dagudu yayi gurin Abokinsa musa yama manta shaf yana makaranta domin yanaimasa gorin kanne mata shi guda biyu yake dasu Raliya yarsheka shidda da Amina yar shekara ukku kofada suke saiyayi masa gori don haka yaga yashiga da ihunsa ko sallama babu yana fadin musa musa zokaga kanwata nima yau Ummanmu tahaifa mana mace mekyau datafi yan gidanku..... Yatsaya turus cike da tsoro sanda lami tafito daga daki tana muzurai kamar zata cinyeshi danye cikin tace shege meyakawoka gidanmu tsinanne yatsaya jikinsa yana kyarma bakinsa yana rawa yace daman..... Daman um Ummarmu ce tahaifi diya mace shine nazo nagayamasa takara dokamasa tsawa kaitafican banza shege ummanku ko ko ummansu kana murna anhaifi mace agidan wasu ko shashasha da baisan ko shi waye ba shege
32 fice kabani guri kuma kaje kasanar da uwar rikon naka inci ubanka shege yajuya yafice dasauri jikinsa yana rawa yana jujjuya maganganunta aransa yakasa fahimtar abinda take nufi sukaci karo da musa azaure yakalleshh yana fadin Ashe ummanku tahaifi mace yanzu rabi.u yake gayamin Awaje yadaure yayi yar dariya ainashiga nagayama banganka ba dokin yarbudurwa yamantardashi Abinda innar musa tayi masa Ranar da hjy Amina tazo barka ranar kwana biyar da haihuwa sanda zata tafi mlm sulaiman yashigo dakayan lambu masu yawan gaske dayake sana.arshi kenan suyake saidawa kasuwar yankaba shagone dashi babba yasamya akadibarmata mai yawa tace yabarshi yace saita tafi dashi saidai motar haya tazo gidan domin motarta tana wurin gyara Ahmad yadaukar mata kayan yakaimata bakin titi suna tafe suna hirar makarantarsu dasauran Abubuwa saiyace mata Anti daman inason Intambayeki wani abu tatattara hankalinta agurinsa tace masa Uhum inajinka yagyara kayan dake kansa yace wai meye shege da Uwar riko kuma? Hjy Amina taja wani wawan birki tatsaya cike datashin hankali tace kai waye yake gayama wannan maganar badai ummar kaba ko ganin

tarude yanda ummansa tayi idan yasanar mata yasanya gabanshi faduwa dan Allah kada kigayawa ummana zatamini fada daman Innarsu musa ce take gayamini kuma canake wani abune mai Amfani shine nake tambaya tayi ajiyar zuciya don zatonta deeje kefada masa haka tace lallai ta cika munafuka tunda take nuna batason kowa yanuna masa ba itace tahaifeshi ba amman duk da haka har lokacin ranta abace yake ta daure tace Agaban ummarka take gayamaka haka kuma yagirgiza kai yana fadin a.a saidai idan nashiga gidanta kuma ummana ma tahanani shiga ranar suna yarinya taci suna Asma.u sunan da deeje kenacin idantahaifi mace asanya mata saboda kaunarta ga mahaukaciya babar Ahmad tun washe garin suna tafara kiranta da ma'u kwanakinsu goma da haihuwa Hjy Amina tayomusu Asubanci sundan tsorata daganinta dasassafe amman ganin tanata wasa da dariya dayara yasanya suka fahimci ba wani abu ne yafaruba saida yaran suka wuce makaranta sannan suka kule adaki aka kara gaisawa suka nutsu sunajiran abinda ketafe da ita tagyara zama tace tabbas kunzama iyaye nagari masu rikon Amana kuma kuncancanci kuyi rainon kowane irin da banzo amatsayin shugabar gidan rainon yara ba domin nayi ritaya saidai nazo amatsayin inakaunarku dason danku Ahmad inafatar idan nafadamuku dalilin dayasa nakeson amsarsa bazaku bata rankuba tunda tafara magana suke kallonta jintazo wannan gaba yasanya deeje mikewa tana fadin tafdi jam ai wlh bazai yiwu ba koshugaban kasa bai isa ya.amshi Ahmad ahannunaba clkin matukar tashin hankali da kuka take maganar shikanshi malam din yakadu dayake namijine yasanya yadanyi karfin hali

Yakwantar da kai yanafadin Adokar daukar yara agidan daman tanuna akwai wani lokaci da ake karbar yaro daga iyayen rainonsa ba.asanar damuba ko kuma rainonmu kikaraina kinaganin kinfimu iya raino hajiya takula dayanda suka shiga Rudu daman kuma tayi tunani haka zata faru dantasan yanda suke matukar son yaron takwantarda murya tana fadin kufahimci kamar yadda nasar da ku banzo da sunanan ma.aikaciya ba saidai yar uwa agurinku Ahmad bashida iyayen dasuka fiku saidai inason na rikeshi nawani lokacine har zuwa sanda zai iya daukar kowacce irin magana akwakwalwasa nasan kun san halin matar can Lami kumasha jin irin rigimar da kuke yi da ita akan yaron to abinnata yakiyin sauki donhaka mezaihana kubani aronsa haryagama Karatunsa na University insha Allah sannan nadawomuku dashi gabadaya suka sauka daga kan fushin nasu dansunsan inda maganarta tasanya gaba donhaka sungano magana tafimtar juna takawota mlm yace shin wani abune yafaru takwashe duk yanda sukayi da Ahmad tasanar dasu sanda zai rakata tahau mota sai deeje tasanya kuka tana fadin Ahaf ainasha gayawa mlm maganar nan matarnan batada mutunci wlh bazan yadda ba Hajiya kiyi hakuri wlh bazan iya rabuwa da Ahmad ba sai inmutuwa ce tarabamu kifahimci Abinda nake nufi Deeje bawai zankwacemiki Ahmad bane dawata manufa hjy Amina tafada da lallashi ganin yanda duk Deejan tabirkice mata mlm ne ya raba gardamar dafadin ke hajiya kiyi hakuri dan wlh rabamu da Ahmad babbar matsalane sannan hakan ma zai iya tona Asirin dakike son Rufewa indai lami ce matsala to zanyi maganinta ayau ba sai gobe ba dakyar suka shawo kanta ta amince zata barshi amman dole tace taza yiwa Lami kashedi da barazana don haka tare suka shiga gidan Lami da ita lami tamike jiki yana rawa tashimfida musu tabarma dan Allah yayita datsoron Hukuma tasan tsaf za.a iya daureta hajiya ce tafara magana cikin bacin rai kinfi kowa sanin laifinki bawai rarrashinki nazo yi ko rokon kiba a.a umurni ne nake baki abinda kikayiwa yaron nan yasarnar damu cikin rawar murya tace wai menayi mlm sulaiman ya yunkura da bacin rai zaiyi magana hajiya Amina datakatar dashi takalli lami tana fadin Kinmance sanda

yashigo gayawa abonkinsa musa haihuwa abinda kikace to zakiyi bayani agaban hukuma tunda tunaninki rashin mutunci saita mike tsaye Hankali jibirilu yatashi yamike dasauri yana fadin a.ah hajiya baza.ayi hakaba tabbas tayi kuskure ayimata afuwa dan Allah yaya kasanya baki Lami kuwa tuni tafashe dakuka tagigice mlm sulaiman yayi dariya aransa yana fadin fitsarar riyar banza saida suka wanasu sannan tayadda tajanye sanarda hukumar yansanda wannan tasanya tadaina kiran Ahmad da shege koda sunhadu ahanya bata kyarar sa saidan harara kawai gabaki daya yaran sundauki soyayyar su sundora kan ma.u shekarunta biyar akasanxata aprimary saidai kullum sai dai kullum sai anyi dambe da ita kamar dage yawanfadan dasukeyi da raliya yasanya ummansu tayimasa kashedi akanta don kullum
Dan kullum Lami ahanyar kawo kara take tayita zage zage da gore gore kalala dole tasanya yadaina kulasu Rayuwa yin Allah ayanzu haka Ahmad yana BUK takano inda yake karatunsa akan computar science Sani kam diploma yayi anan FCE sai yayi sa.a yasamu yasamu aiki awani kamfani maizaman kansa shikuwa Auwalu makarantar aiki tsafta yayi HND yabude chemist anan jikin gidansu yakuma samu aiki a temprary rabi u kam yanbokone nahakika ma.u kam ana aji daya a secondary school saikara firirita ake da iyayi da gwalli tafi kowa kokari a ajinsu gaba daya kai harma acikin tsaran ajinta itace kedaukar na daya wannan yake karamata soyuwa awurin yayyanta kafin ummansu ko babanta yayimata abu daya sunmata goma dominshi idan yatashi saiya hada dasu Raliya danhaka tafisu komai Raliya datake ganin itace budurwa dayadace tayi kwalliya sai taga ma.u tafita dawani yammaci lokacin ma.u tadawo hutu domin makarantar kwana take tataso daga islamiyya tana rike da kur.ani tahango lariya taci kwalliya tanufi shagon sisko wani dangayene a Unguwartasu da inmace kekulasu ake ganinta mara kamunkai dan haka tanaganin Raliya tashiga shagon sisko jikinta yadauki rawa hankalinta baikara tashiba saida taga saida ta hango sisko yadan leko yakalli gabas da yamma sannan yaja kofar shagon nasa dasauri ya kulle tayi dum dum cike da tsoro da fargaba tayi hanyar gidansu dasauri tasanarwa da yayyanta tayi sa.a ta tadda Ahmad da musa akofar gida zaune suna hira jikinta yana rawa idonta nazubda hawaye tanufesu Ahmad ne ya farga da ita yakalleta da mamaki yana fadin yadai ma.un baba lfy cikin rawar murya tace Raliya Raliya ce tashiga dakin sisko suka mike atare arude suna fadin Raliya zomuje saidai wani Abin bakinciki sanda suka isa kofar shagon suka hango cincirindon mutane ashe wani saurayi yaga sanda tashiga darufe kofar da akayi ya gayyato wasu matasa aka balle kofar dakyar suka barta tadaura zani suna mata ihu suka fito da ita tanufi hanyar gida tana kuka shikuwa sisko rufeshi sukayi da duka Ahmad da musa suka isowurin cike da bacinrai tundaga nan suka zare belt dinsu suka fara narkarta tana ihu tanufi gida da gudu Ahmad yarufamata baya shiko musa takaici ya isheshi yaga garayaje yakoyawa sisko hankali tashiga gidansu dagudu tana ihu daga itasai daurin kirji yankayanta data dauko duk tawatsar dan zafi duka yabita hargidan nasu yana dukanta tana ihu lami tafito daga daki arude tana fadin meyene yake faruwa tatsaya turus ganin Ahmad nadukan Raliya har cikin gida wata zuciya ta ciyota ta isa dasauri
35 ta angajeshi tana fadin shege dan iska mediyata tayimaka dazaka biyota kana dukanta tamike cike damamakin ganin diyar tata daga ita sai daurin kirjg Ahmad yamike yataso daga cikin kwanikan wanke wanke data hankadashi yana karkade jikinsa ya isa kusa da ita yana fadin inna wannan yarinyar yau ta tona asirin gidannan ta tozartamu ashagon sisko aka kamata yara suka rakota suna mata ihu meyafi wannan takaici da tozarta sunan gidannan yakarasa maganar da kunan rai Lami takalleshi cike da wani irin bakin ciki data kasa rikewa tace Ahayye

yaufa karin maganar hausawa tafito SHEGE YANA YI DAMAI ZINA don ankama Raliya ashagon sisko zaka biyota kana mata wannan dukan kaine kafi cancanta da adaka ba Raliya ba Shege irinka ne zaitonawa maiyin zina asiri cikin tada jijiyar wuya take magana musa dayashigo bakomai ahannunsa ya isa cike da bacin rai dadamuwa ganin yanda Ahmad ya tsaya sororo yana kallonta cike da madaukakin mamaki donshi sam baifahimci tana daurewa diyarta gindi ne akan abin da ta.aikata musa ne yace haba inna baidace kidaurewa yarinyar nan gindiba har kidinga ciwa Ahmad mutunci ba kai rufemin baki da.ace kai ko Auwalu ko sani suka kamo yarimyar nan dawani banzan damuba tunda ku kowa yasan "ya"yan halak ne ba shegu ba amman wannan yaron shege ne zai aibata diyar da akahaifa tahanyar Auren sunna ta Nuna Ahmad gaba daya suka tsaya suna kallonta cike da fargaba tashin Hankali musa yafara magana cikin kaduwa da gigita inna kazafi baida kyau kada tunanin nemawa Raliya kariya yasanya kifita daga haiyyacinki harkije ki fadi abinda baidaceba ninasan Ahmad dan gidan baffa sulaiman ne kuma...... Kai tafi can toyau zanfasa kwan da.akajima ana kiwonsa yau zansanarda kai abinda bakusaniba saunawa nake gayamuku kudaina damuwa dan Ahmad yafiku wani abu kasha damuwa danyafika kokari kasha damuwa danyafika kaya nasha gayamaka duk dayafika aikin banza ne tunda ku kunada abin ado wato uba shikuwa shege ne dan mahaukaciya wacce ba.asan daga inda ta fitoba ........ Innalillahiwainna ilaihi rajuun lahaula walakuwati illah billah muryan Ummansu Deeje ta ankardasu wacce ta shigon gidan gigice jiyo hayaniyar da akeyi taleko taga abinda ke faruwa Ahmad kam mutuwar tsaye yayi yakasa motsawa daga inda yake tabbas yasha tunanin maganganu Lami dake fada akansa Ummansa da Hjy Amina suna tauye masa tunaninsa wannan ne yasanya hankalinsa ketashi aduk sanda sukaji ance masa shege faduwar da Ummansa tayi jib dafasa ihun ma.u ne yadawo dashi cikin hayyacinsa

Yanufeta da gudu kamar yanda yaga musa yayi idonta yabirkice yajuye da alama banumfashi a tattare da ita cikin karaji ma.u kefadin umma kada kimutu kibarmu dan Allah Umma kitashi shikam gaba daya tunaninsa da basirar sa suntushe yakasa cewa komai sai hawaye da idonsa keyi musa ne yamike dagudu yadebo ruwa abuta ya yayyafa mata amman abanza bata ko motsi sai asannan ya iya bude baki yana fadin Umma kada kimutu kece Uwata maisona idan kika mutu zankasance banida kowa kitashi Umma kici gaba darikeni a matsayanin danki na cikinki kada ki mutu Umma na yana kuka da majina yake wannan magana musa ne yayi dabara fita dagudu yanufi gurin Auwalu dake chemist wanda bai san wainar da ake toyawaba Lami kam tayi tsuru tsuru tsaye da fargabar da tashin hankalin abinda zaije yazo Raliya kam sai sharbar kuka take yi cike da takaici da dana sani Auwalu yashigo aguje hannunsa rike da fanfon auna jini ya isa gurin mahaifiyar tasa yahada bakinsa danata yafara bata taimakon gaggawa da ake kira da mouth to mouth yatallafo kanta cikin ikon Allah saiga numfashin nata yadawo tabude idonta dasauri saita mike zaune kamar ba itace tasuma ba yanzu takamo Ahmad tana fadin karya take nice nahaifeka ba mahaukaciya ba ranar dana haifeka ne tazo nan gidan katambayi malam kaji ainasha gayamaka Lami makaryaciyace tana kuka take maganar shima Ahmad kuka yakeyi Auwalu da baisan abinda ke faruwa ba yamike cike da mamaki yana fadin wai meye yafaru me yasameki Umma? Arude yake maganar saita mike cikin karfin hali tana fadin babu komai kuzo muje gida banason kara kallon fuskar Azzalumar matarnan tanuna Lami da hannunta Ahmad yarirriketa dakafarsa suka nufi gidansu harlokacin musa Ahmad da ma.u kuka suke Lami ji take yi kamar maganar tadawo tamaidata cikin ta donbatasan abinda zaibiyo baya ba amman saboda tsabar taurin rai saida taga sunfice eh gaskiya ce nafada sai dai Akasheni

wallahi haka kawai shege zaitonawa diyata Asiri yanda yatona m
ini asiri nima natona masa
37 koda suka iso gidan abin datake maimaitawa kenan Auwalu yace Umma mema tacene? Meyafaru ne? Cikin kuka tace Azzalumace Lami waicewa tayi Ahmad shege ne bayan nice nahaifeshi da cikina cewa tayi dan mahaukaciyane bayan gashi dana ne ranar dana haifeshi ranar mahaukaciya tazo nan gidan bari kuganima na dauko muku takaddar dazaku san danane saita mike jiki yana rawa takama lalube saidai abinda batasaniba shaidar datake son kare ta itace zata kara sanyawa abin yafito fili tunda duk mutumin dayakasance danka dakahaifa aibabu bukatar wata shaidar takarda arubuce gashi ita batasan abinda akarubuta na yarjejeniya bace baiwar Allah saida tafito dakayan wata tsohuwar adaka sannan takwakulo wata takarda acan kasan jikinta yana rawa tamikama Ahmad tana fadin karanta kagani karya takeyi nice babarka ya.amsa yafara karantawa bawani abu Acikiba illah yarjejeni sun amsheshi zasu rikeshi kuma duma duplicate ce aka basu da.alamu original din tana can inda suka basu shi kukansa yakuma karuwa hankalinsa yakuma tashi tabbas ba sune iyayensa ba Auwalu ya warce takardar yafara karantowa yakalli mahaifiyar tasu datausayi datashin hankali rashin ilimi datayine yasanya batasan Abinda takardar takunsa ba data sani data kara boye takardar cikin sheshshekar kuka yake fadin Umma wannan takardar tana nuna yarjejeniya dakukayi ne asanda zaku amshi wani yaro nasan ba Ahmad bane mantawa kikayi kika fito da ita sai asannan tagano wautar datayi amman taji dadin yanda Auwalu din yakawo mata mafita dasauri tace ahaf namanta wannan ajiya ce akabani bari nazakulo wancan bani na adana wannan din kafin masu ita suzo nema ta.amsa dasauri tanufi akwatin tana cigaba dalalube tsanananin tausayin dasoyaryar Ummansu tashigeshi yakula da idan baiyi wani abuba zata iya rasa hankalinta ko wani yashigeta yanufeta inda take tazakulo kaya daga cikin tsohuwar adakar yadafa bayanta yana kokarin kwantar mata da hankali yace Umma kidaina lalube nifa nasan kece mahaifiyata bakece kikasha gayamin innarsu musa karya ne da ita ba tayaya zanyadda damaganarta dake ba uwataba ce ba saikin nunamini watarana dakuma saiwani yayi mini gori acikin layin nan kishare maganarta ki kwanta ki huta tana son bata miki raine don ankamo diyarta dakin sisko suna iskanci tadago cike da matsananci farinciki tana fadin haba ainasan saboda mugunta take son rabani dakai tahadda samaka wani ciwon dazan rasaka bakayadda da abinda taceba kenan? Yadaga mata kai yana kokarin kakalo murmushi wannan yasanya tadan sami sassauci aranta daga wannan karon anyita takare ko ita ko lami dole dayan yabar gidan dakyar ta iya kyalesu suka tafi masallaci bada farali gani take yi kamar daga can bazata koma ganin Ahmad dinta ba saidai shi yana sallah yana kuka ransa yayi baki ashe shi yanata barankadama da homa ashe shi shege ne bashida kowa aduniya shin wacece mahaifiyarsa datayi shegensa koda yake ance mahaukaciya ce to waye mara imani dayayi mata ciki har kawo shi duniya
38 tana ina ita mahaukaciyar ta warkene kohar yanzu tana cikin haukan? Yakasa natsuwa daga masallaci yalallaba yafice yayi gabas yana ta tafiya baisan inda zaidosaba Anshirya cin abinci yanda aka saba amman babu Ahmad tun Ummansu nasanya rai zaishigo har tafara karaya bacin rai datake kokarin boyewa yafara yabaiyana tadinga sanyawa ana nemansa sam tahana kowa cin Abinci nan malam yashigo cike da taikaci yana fadin wai Ahmad yaro ne dazaki sanya ayi ta wani nemansa saika ce wanda zaibata kinsa dai bazai wuce yana gidan yaron Abokinsa Abdullahi ba cikin sheshshekar kuka basan abinda nasaniba tabbas idan Ahmad bai bata ba to

zaigudu kuwa saita fashe dakuka cikin mamaki yakd kallonta hasken wutar lantarki da.aka kawo yanafadin wace irin magana kike yi khadijatu kamar wacce tayi gamo memukayi masa da zai gujemu cikin kuka tace yau Lami tasanar da Ahmad shi shege ne tasanar da shi banice nahaifeshi ba tagayamasa shidan mahaukaciyane baniba... Kuka take yi sosai kamar wata karamar yarinya malam yamike cikin tashin hankali yana fadin mekikeson sanar dani khadija inanilillahi wainna ilaihi rajuun yanzu ina Ahmadu bari nanemoshi... Baijira yi jin abinda zatace ba ya fice sani da salisu da rabi.u ne agurin sunkuma riga sun fahimci abinda ake anufi saidai harkarfen dayan dare babu Ahmad babu labarinsa hankalin kowa yatashi sanda malam sulaiman yashigo gidan Umma Deeje tamike tana fadin yaya dai malam kungan shi yagirgiza kai cike da damuwa mai tsanani takuma wurga masa tambaya hargidansu Abdullahi mlm kunje munje taredashi muke ta nemansa ma yanzu haka nabarsu shida Auwalu suna ta bin gidajen Abokanansu Akanme zaku wahalarda kanku wanda yabata ake nema bawanda yagudu ba Ahmad bazaije inda zaku ganshi ba abinda najima ina nusar da kai kenan wlh Lami bamasoyiyar mu bace ko Ahmadu yadawo ko baidawoba nagama zama a gidannan yanda Ahmad yatafi haka nima zatasalwantar min yarana tana magana tana kuka ya hasala matuka gaya yama rasa hukunci dazaiyanke sai kawai yamike cikin fushi yanufi gidansu Lami Yanashiga yakama kwada sallama kamar zaitsaga gidan dafarko sunyi shuru adaki don lami tagayamasa tabargazar dayayi duk da lika abin asharri yayiwa diyarta ammam duk da haka mijin nata yabata rashin gaskiya don yana tsoron abin da zaije yazo can dai sai ga mlm jibiril yabayyana cike da tsoro mlm sulaiman yagalla masu harara yana fadin Barkanku Ahmad yagudu yabace mana yarabu da mu saidai kusani jibril yanda Ahmad yarabu damu tokaima karabu da komai nawa kashirya kayanka agobe zansanya gidan kasuwa tunda dai zamanmu tare baida Amfani sai haddasa masifa nima nahakura dazaman gidan gabadaya hankalin jibril yatashi idan yarabu dan uwansa inazaisoma rayuwarsa waye zai iyaciga dabashi taimakon dayake bashi tabbas shikansa yanzu lami ta isheshi yabi dan uwansa yana bashi hakuri amman ina tuni yafice yadawo tsakar gidan yayi duru duru cike da tashim hankali saiyafada dakin dasauri yatadda lami zaune tayi wuki wuki tana zare ido yana shiga tafara magana ka kwantar da hankalinka malam indai akan gidane muje mukama haya tunda ai....... Rufemin baki munafuka sau nawa nake cemiki kicire hannunki daga kan maganar yaran nan yaji koshi waye aduniya amman saida kika fadamasa to tsaya kiji banida wani gata dayawuce na Allah da dan uwana daya daukoni daga cikin wahala yanemo mini aurenki yaci gaba da dawainiya dani kisani idan na bar nan banida wurin zuwa don haka kedai da kika janyowa kanki kece zakibar gidan dolenki kuwa takalleshi damamaki matuka tana fadin malam akanfadin gaskiya kake wannan furucin kinga banja dagon zance dakeba kiwuce kawai nasakeki yana kaiwa nan ya fice daga dakin .......40 Lami tafashe da kuka tana fadin na shiga ukku yanzu akan dan shege har akasane natsani wannan yaro daman nasan zuwanshi gidannan Annoba ce kuma harzuwa yanzu banyi nadamar fadin cewar shi shege neba dawannan tadinga sambatu tana kuka Sunwayi gari cikin tashin hankali kam tun Asuba tabar gidan saboda yanda jibril ketayimata kwakwazo hankalin yayanta yatashi matuka musamman Raliya da Amina musa kam yanajin ciwo sakin mahaifiyar tasa Amman yanajin takaicin Abinda ta.aikata gaba daya gidan angaza karyawa kowa yanacikin damuwa ma'u kam kuka takeyi tana fadin danasani dabangayawa yaya Ahmad abinda raliya keyiba duk da deeje tana cikin tashin hankali hakan baihanata rarrashin diyar tata ba tunda suka dawo daga masallaci jibril yatare malam yana kara bashi hkr

dasanar dashi hukunci daya yanke tun dare jiya malam sulaiman yakalli dan uwansa cike da tashin hankali yace subhanallahi meya sanya ka.aikata haka nima bacin raine yasanya fadin abinda nafada kayi hakuri da abinda nayimaka dankai dan uwa nane jinina daban isa nasakakaba Dejee kam bataji ko dar da mutuwar auren lamiba tunda tarasa danta komaima yafaru wajen misalin karfe goma sai Hajiya Amina ta iso akidime don yan dubo Ahmad sun iso hargidanta duk yanda deeje kekorin taddanne zuciyarta saida ta fashe dakuka ganin hjy Amina tana fadin yagudu hjy bamusa inda yashigaba danasani munbakishi ina zankai hakkin yaron nan tadafa kafadarta cikin kwantar da murya take fadin kidaina wannan maganar deeje ko ina yake aibazaiwuce kaddararshi ba Nakuma tabbata duk inda Ahmad yake zaidawo inda kuke muyi Addu.a kalaman hjy ne suka dan kwantar mata da hankali tace kuma adaina zuwa nemansa zaidawo dakanshi tasoyin maganin lami saidai tasamu Ibr sakin da.akayimata kwanaki ukku suka cika cikin tashin hankali abincin kirki babu maici agidan Ranar kwana na hudu datafiyar tasa ma.u tadawo daga kai markaden gero na kokon da yamma sakaliya tana tafe tarera wakokinta tahangoshi tafe da kayansa tunna ranar dayatafi yarame yayi duhu dakyar yake tafiya kamar me ciwon kafa batasan sanda ta watsar da robar markadan ta falla gida dagudu tana fadin Umma gayaya Ahmad umman dake tukin tuwo tafito da.azama jikinta sai kyarma yake harzaninta yana neman faduwa darawar baki tace A ina kikanshi gashinan zaishigo gidannan yashigo gidan dasallama

41 yatsaya turus cikeda farin ciki ganin ummansa itama tsayawa tayi turus tana kallonshi kuma kome tatuna saita nufeshi da sauri ta wanka masa mari sai kuma tafashe dakuka tajuya gida da sauri ma.u dake tsaye ta zuba masa ido wanda ya ciko da kwalla shima idon ya zubamata yana hawaye shida kansa yasan abin da yayi bai kyauta ba cikin kuka tace yaya Ahmad mai yasanya ka gudu ka barmu Umma ta daina bacci tadaina cin Abinci baba yadaina fita kasuwa yaya Auwalu yadaina zama a chemist sani yadaina zuwa kasuwa ni idan akaturani makaranta bana zuwa sai intafi nemanka ranar har gwammaja naje dakafuna nemanka memukayimaka kagudu kabarmu yakamo yarinyar maicike dawayo ya rungume yana kuka yafadin ba gudowa nayiba tafiya nayi nasamu natsuwar zuciya ta saidai bansamuba zama daku shine nutsuwar zuciyata yamike hannunta suka nufi cikin gida saidai duk yanda yaso yayi wa Umma magana taki sauraronsa tayi fishi dashi maitsanani wanda yakara tada masa hankali Malam sulaiman yagyara zama yana fadin tabbas hjy Amina tayi gaskiya tace mini Ahmad bazai iyabarinmuba munyi masa rikon dako mahaifiyarsa ce tadawo duniya bazatayimasa irinsa ba saidai nayi mamaki dakabarmu Ahmad shinkanaganin kayimana adalci yadukar dakai cikin kuka yake fadin kuyafemin baba tabbas nasan na.aikata muku laifi mai girma wani irin tausayi yakama malam mai tsanani shikadai yasan Abinda yakeji Azuciyar sa game da yaron

42 kwanaki sunja ga Lami tun tana ganin abin kamar wasa har karamar magana tazama babba domin sam mlm jibril yaki zuwa biko sai abin yazamomasa kamar gaba takaishi domin daga gidan yayansa yayansa akefitomasa da girki maidadi wanda yafi namatar sa Su raliya kam kullum saita saci jiki ta tafi gurin uwarta suyita ta kitsa mugunta dadai lami ta kula abin bana wasa baneba hankalinta yafara tashi ga wahalar gidan tafara damunta da yunwa don haka tafara bin kan mahaifinta

DAME AKE ADO PART 4

Saidai mlm jibril yace bashi za.aba hankuriba yayansa za.aje abaiwa idan yahakura shikenan

dan bawan Allah baiyi kasa agwiwaba yanufi gurin mlm sulaiman din darajar tsohon tasanya yace shikenan komai yawuce amman sujawa Lami kunne matuka domin bazasu kuma yadda da irin wannan rashin tarbiya ba haka tsohon yatafi yana godiya haka aka tarkato Lami aka dawo da ita su Raliya tamkar sallah shi kuwa mlm jibril sai cika yake domin wahala takuma dawo masa sabuwa dal yanayin Rayuwar Ahmad tasanya gaba daya yadukufa kan karatunsa bashida lokacin komai sai karatu idan kaga yana dariya yana cikin gidan donka da Ummansa ta damu ahaka har suka shiga aji hudu Ummi sada itace yariyar data dafe masa tun farkon shigowar su take bibbiyarsa dafarko dasigar koyon karatu tashige shi har shakuwa tashiga tsakaninsu ahankali tajuya soyayya kusan kowa yasan halin da ake ciki cikin dakinsa ma katon hoton tane kyakykyawa ce fara da ita duk da bata cika tsayiba Ummi ce kadai kesanyashi farinciki idan yana cikin damuwa yana son Ummi matuka musamman yanda iyayanta suka daukeshi kamar su suka haifeshi yana tsaye adaki yana kallon hotonshi na ranar dasuka kammala karatu yana sanye da kaya wadanda digiri yan uwansa sun baibayeshi cike da farin ciki ga hajiya Amina agefe dakuma babansa ga ma'u nan anyimata kwalliya yana matukar son hoton arayuwarsa domin yasanshi dangata ne lokuta dadama kalmar shege tafado masa yatuna wannan matsayin dayake kai yakuma tuno yanda yan uwansa da iyayensa kesonshi sai yaji zuciyarsa tayi wasai baitaba kukan rashin dangiba sakamakonsa yayi kyau matuka har an turashi jahar taraba bautar kasa hankalin Ummi gabadaya yatashi domin batason yayi nisa da ita aganinta shekara tayi yawa saida yadinga tausarta dasu ishak sannan tahakura itakam tayi sa.a batayi nisa ba jigawa akaturata amman bakincikin rabuwa damasoyinta yaraunana farincikinta kwanci tashi kamar yaune shekara guda sai gashi haryadawo umma tayi murna matuka hajiya Amina kamar itace tayo sabon digiri sai murna take yi da Alfari ta amshi takardunsa daniyar tanemasa aiki saidai abin yaci tura domin samun aiki agarin saika shirya daga karshe dai tasamomishi aiki n gidan wani mai dasuke mutunci da maigidanta da maigidan man kwarai dagaske Alhaji nura kwangila yayi murna kwarai da samu don babu abinda yake buri illah yafara cin gashin kansa yataimakawa iyayensa kamar yanda suka yimasa duk sanda yatuno iri dawainiyar dasukayi dashi saiyaji son su yakuma cika ranshi Lami tayi tagama tsakaninta dashi saikallo sai harara domin tunbayan dawowarta gidan tashiga taitayinta saidai samun aikin nasa yatsaya aranta matuka domin cikin kankani lokaci komai nasa yasauya yakuma yama dan gayu cikin lokaci kankani yasayi babur dinsa irin wanda samarin zamani ke yayi tsutsun soyayya ...

44 ba umma ba hatta mlm yadaina kukan babu domin Auwalu da sani da Ahmad sun isheshi kowa akwai abinda yaware yake siya awata don ma dai Auwalu yatattago Aure amman duk da haka yana iyakacin kokarinsa ko kishin yanda rayuwar gidan ke gudana Lami batayi nata sanya yayanta suzama mutane nagari idan kafidda musa saishegen kishin tsiya da kyashi Raliya kam likkafa taci gaba tazama gogaggiyar yarduniya domin duk tayi billicin tayi fari tas kamar gauta ga tara samari kala kala akofar gidan tun yayyen suna fada har sun gaji sun watsar domin lami ke dauremata gindi tace anayiwa hassada dakyashi cikin wannan sati aka kai kayan Auren Ahmad gidansu ummi saidai mahaifinta yatsaida lokacin biki gabadaya wata hudu wannan abin yafi yiwa Ahmad da ummi dadi domin sunkagu sumallaki junansu Abba da umma kuwa sunyi farinciki da hakan Ahmad kam yadage hada kayan Aure sai Alokacin yagano kokarin da Auwalu yayi dominshi har gini mayayi koda yake tuni yazama cikakken ma.aikaci yana da albashi me kyau shi kam haya zaikama dole amman gaskiya ba zai kama hayar karamin gida ba domin

yasan Umminsa yar gayuce gwara ya kama gidan da zaiburgeta saura wata daya biki yagama hada kayan lefensa yayi kokari matuka domin saida yayi akwatuna hudu sanda yakawowa su umma kaya sun cika mamakin kokarinsa daganan yafara kokarin nemo gida da kudin haya dama babansa ya sauke masa sadaki domin tun sanda za.akai kayan lefe yabada dubu ashirin na sadaki biki yarage sauran sati biyu yasami gidan sa makyau acan Unguwar gaida mai dakuna madaidata guda ukku da kichen da bandaki dangin Ummi harsunzo sun gani sunyaba komai gabadaya gidan ansanya masa wuta yaimasa fenti maikyau saidai abinda yafi damunsa da za.ayi bikinsa ma.u bataman domin suna gab dafara jarabawa tunsauran kwana goma biki yafara rabao iv nabiki yabaiwa Ummi nata anshirya shagali daidai na takala ma'u kam harkuka tayi amakaranta domin tana lissafin bikin yayanta yazo saura sati guda biki da magriba Umma tana tsakar gida tana ta aikace aikace mata suka fara shigowa gidan da sallama dauke da akwatuna riki riki mamaki yacikata ta mike tsaye tana tambayar lafiya daga inakuma? Domin tasan basuda wata budurwa daza.akawo kayan aure saida suka gama ajiye kayan babu ko gaisuwa daya daga cikinsu ta kalli umma tace daga gidansu Ummi aka aiko mu mudawomuku dakayan aurenku domin ajiya mukasamu labarin ashe yaron dake neman diyarmu ba danku bane ba shege ne daba.asan asalinsa ba Umma tadafe kirji cike da fargaba daidai lokacin Ahmad yashigo gida inyajikomai akunnensa don haka yatsaya turus a bakin kofa cike da tsananin damuwa datashin hankali MUHADU AKASHI NA BIYU